# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tuntuɓar juna tsakanin addinai: Haɗin kan mutanen Sodangi
## Kashi na tara: Sulhu

Wanda ya rubuta: Romie Singh
Wanda ya tace: Katrin Ogunsade, Naïma Guira
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja

**'Yan Wasa:**

Dauda: ɗan shekara 17
Shugabar makaranta (Madam Titi): 'yar shekara 48
Layla: 'yar shekara 16
Ɗanjuma: ɗan shekara 16
Tafida: ɗan shekara 17
Fada Bana: ɗan shekara 49, kawun Dauda
Malam Isma'ila: ɗan shekara 43, baban Layla
Hassan: ɗan shekara 12
Maigida Ranau Dembele: ɗan shekara 51, baban Dauda
Baban Tafida: ɗan shekara 50

**MAI GABATARWA:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin kashi na tara daga cikin goma na wasan kwaikwayonmu na “Ji Ka Karu” mai taken “Haɗin kan mutanen Sodangi”, wanda aka shirya a kan yadda addini da siyasa suka haddasa zaman doya da man ja tsakanin al’ummomi guda biyu. Kamar yadda aka saba muna tare da taurarin namu, wato Dauda da Layla, da wasu abokanansu. Yanzu sai mu saurari waɗannan taurari namu, don mu ji yadda suka fahimci muhimmancin tattaunawa da haɗin kai da kuma haƙuri da juna. A wannan kashin wasa na yau mai suna “Sulhu”, Layla ta kawo shawarar da take ganin za ta kawo masalaha a rikicin da ake yi a kan filin nan. Ku biyo mu don ku ji ko Layla za ta yi nasara.

**Fitowa ta 1: A ɗakin taron safe a Kwalejin Zumunta**

Dauda, Shugabara makaranta

**MAI BA DA LABARI:**

A wannan safiyar Tafida ya shiga ɗakin taron safe ne ransa a ɓace. Ya tozarta babban abokinsa Dauda a kan yarinyar da bai ma gama saninta ba. Haƙiƙa yana son Layla amma ba tare da ya fahimci ita wace ce ba. Sai dai yana sonta ne kawai saboda kyanta da ɗabi’arta da kuma basirarta. Bayan shugabar makarantarsu ta kammala karanta addu’ar wannan safiyar, wadda wani mai bin addinin Buda ɗan asalin yankin Tibet ya rubuta, wadda ta yi tasiri sosai a kansa. Nan da nan sai Tafida ya fahimci kuskurensa, sannan kuma ya fahimci cewa lalle da sauransa a rayuwa.

**SHUGABAR MAKARANTA:** Ɗalibai, mu yi addu’a.

> *Ita rayuwa, ya wajaba ku fahimta, kamar ɗugon ruwan sama ne.*
> *In dai ana maganar kyau ne, to yakan gushe ne kamar ba a yi shi ba.*
> *Saboda haka, ya kamata mu zama muna da manufa.*
> *Mu yi abin da zai amfane mu dare da rana.*

Irin waɗannan tunane-tunanen da sanyin safiya, su suke taimaka mana mu yi kyakkyawan tunani game da rayuwarmu, mu kuma ɗauke ta da muhimmanci, da kuma yadda ya kamata mu gudanar da rayuwar tamu. Mun ga illar rikicin addini a wannan nahiya tamu. Mun ga yadda aka yi ta kashe-kashe da ƙona masallatai da coci-coci, duk wai da sunan addini. Mu a nan garin Sodangi muna so mu tabbatar da cewa akwai mafita ga kowane irin rikici ta hanyar tattaunawa da 'yancin musayar ra'ayi da kuma shugabanci mai ma'ana. Yanzu an ba da shawarar cewa a yi bikin Ranar Sabunta Zumunta a wannan gari na Sodangi nan da wata uku. Saboda haka, hukumar wannan gari za ta gudanar da wani biki na kwana biyu da kowa zai halarta. An kuma gayyaci dukan makarantu su shiga. Za a yi gasar muhawara, da ta wasannin motsa jiki, don mu taya manyanmu na gobe murna. To, Allah ya ba da sa'a!

**Fitowa ta 2: A Kwalejin Zumunta**

Dauda, Ɗanjuma, Tafida, Layla, Shugabar makaranta

**DAUDA:** Ɗanjuma, Layla ta ƙi kula ni fa!

**ƊANJUMA:** Haba Dauda, tana fushi da kai ne a kan wani abu ko?

**DAUDA:** Rashin fahimtar juna ne kawai a kan abin da bai kai ya kawo ba! Kai! Ga Madam Titi nan ita da Layla, kuma nan suka nufo!

**ƊALIBAI:** Madam, ina kwana?

**SHUGABAR MAKARANTA:** Yaya dai Dauda… Ɗanjuma… Tafida… Akwai wata kyakkyawar shawara da Layla ta kawo min game da Ranar Sabunta Zumunta. Yi musu bayani, Layla!

**LAYLA:** E to, me zai hana mu gudanar da gasar nan da za a yi ta kwana biyu a filin nan da ya haddasa gaba tsakanin al'ummomin nan namu, da iyayenmu. Ko yaya ka gani, Dauda?

**DAUDA:** Ba shakka Layla, wannan shawara ce mai kyau!

**ƊANJUMA:** A matsayin wani matakin sulhu ko? Wannan tunani ne mai kyau!

**SHUGABAR MAKARANTA:** Tafida? Yaya ka yi shiru ne? Me ka gani? Babanka zai iya ba da muhimmiyar gudummawa cikin al'amarin a matsayinsa na editan Jaridar Muryar Sodangi.

**DAUDA:** Kina ganin zai ɗauki nauyin buga wannan abin a jarida?

**TAFIDA:** In dai manufar ita ce a hana mabiya kowane addini mallakar filin, na tabbatar zai yarda. Zan yi masa magana.

**SHUGABAR MAKARANTA:** Amma fa ka sani har yanzu kowa a ciki yake da kowa. Kana jin a irin wannan yanayin akwai yiwuwar sulhu? Ko me ka gani Dauda?

**DAUDA:** Da ma ni ina ta ƙoƙarin shawo kan kawuna ya yafe wa Hassan, ya kuma janye ƙarar da ya kai wajen 'yan sanda.

**LAYLA:** Allah Dauda? Da gaske kake? Na gode, Dauda!

**ƊANJUMA:** Amma kuma ya kamata a hukunta duk wanda ya cinna wutar nan fa.

**DAUDA:** Haka ne. Da ina tunanin ko a sa shi ya yi ɗan wani aiki maimakon horo. A iya sa Hassan ɗin, ko ma dukanmu gaba ɗaya, mu share cocin.

**TAFIDA:** Kai! Ya kamata mu faɗi abin da zai yiwu. Ba na jin zai yiwu ka sa matasan Musulmi su share coci.

**LAYLA:** Me zai hana, Tafida? Mu sa su mu gani mana! Ba ta haka za mu fara tattaunawa ba?

**DAUDA:** Mhm. Ni fa ina ganin share coci abu ne na ɗan lokaci. Me zai hana mu kafa wata cibiyar matasa da za mu dinga yin wasanni gaba ɗayanmu.

**SHUGABAR MAKARANTA:** Mhm.... wato cibiyar ta ƙunshi masu al'adu dabam-dabam ko? Wannan shawarar ta kwanta min! Amma mu yi abin bi-da-bi. Sai mu fara tuntuɓar waɗanda abin ya shafa, kuma in za a yi sulhu sai an tara waɗanda abin ya shafa.

**LAYLA:** Zan so a ce ni da Dauda mu muka fara ƙoƙarin shawo kan iyayenmu su haƙura da fafutukar da suke yi ta neman filin nan, su bar wa hukuma ta yi amfani da shi don abin da ya shafi al'umma.

**TAFIDA:** Ni kuma zan faɗa wa babana tun da lokaci ya yi, da ya kira taron sulhu a cikin sharhin jaridarsu.

**ƊANJUMA:** Ni kuma zan taimaka na sami ɗaliban makarantar Islamiyya don mu ga ko za mu iya haɗa kai mu yi aiki tare. Ba wai na wani ɗan lokaci ba.

**DAUDA:** Zo mu je Layla. Ya kamata na yi miki wani bayani. Mu je kusa da kogi ƙarƙashin gadar Sodangi.

**Fitowa ta 3: A ƙarƙashin gadar Sodangi**

Dauda, Layla

**DAUDA:** Yauwa, ga shi har mun iso! Ba wanda zai gan mu a nan! Yauwa Layla! Don Allah faɗa min me ya sa ranki ya ɓaci bayan an tashi daga taron Kungiyar Muhawara?

**LAYLA:** E to, uhmm... ina jin dai kishi ne ya lulluɓe ni! Saima ce ta faɗa min Maryam tana sonka. Kuma in har ta ba ka kuros...

**DAUDA:** Haka ne. To dai tana so ne ta sa na zama ɗan ɗariƙar cocin Rabaran Haruna Emah, amma gaskiyar magana, tun daga ran nan ban sake komawa takan harkar ba. Sai kuma Tafida da ya ƙarɓi kuros ɗin. Ina jin daga aljihunsa ya faɗo.

**LAYLA:** To Tafida! Ina jin akwai abin da yake damunsa. Ka ga, duk mu manta da kome. Akwai wasu muhimman abubuwan da ya kamata mu mai da hankalinmu a kai.

**DAUDA:** Haka ne! Yanzu ni da ke sai mu je mu sami Kawu Fada. Sannan sai mu tafi wajen babanki.

**LAYLA:** Kullum babana yana mamakin abin da ya sa Hassan ya jefa bom ɗin fetur a cocin nan fa! Na san zai so a yi sulhu tsakanin gidanmu da naku.

**DAUDA:** Sannan da mu ma? A sami zaman lafiya ko?

**LAYLA:** Zaman lafiya da ƙaunar juna, Dauda.

**MAI BA DA LABARI:**
Ga su can! Shi ke nan! Tafida ba shi kuma da wata dama ta samun biyan buƙatarsa dangane da Layla, kuma a hankali har ya fara haƙura. A halin yanzu kuma, Fada Bana ya fara gano tasirin zumunta a cocinsa.

**Fitowa ta 4: A coci**
Fada Bana, Malam Isma'ila, Hassan

**FADA BANA:** Malam Isma'ila! Kai Hassan, me ya kawo ku cocina?

**MAL. ISMA'ILA:** Yi magana mana, ɗana.

**HASSAN:** Fada, na zo na ba ka haƙuri ne a kan abin da na yi. Ka yi haƙuri don Allah!

**FADA BANA:** Uhmm...haƙuri... To, shi ke nan.

**MAL. ISMA'ILA:** Fada, dukkaninmu mun yi imani da Ubangiji ɗaya. Mu muna kiransa Allah kuma shi mai gafara ne ga mabiya addinmu da naku. Haƙiƙa ɗana ya yi nadamar abin da ya aikata. Kuma duk abin da ka sa shi zai yi. Ni ma a matsayina na ubansa na amince da haka. Sannan ina mai tambayarka da me kake so mu yi don mu sasanta tsakaninmu?

**FADA BANA:** Uhmm...to. Bari mu yi addu'a! Mu durƙusa kuma... duk mu ɗaga hannunmu mu nemi jin ƙan Ubangiji ta hanyar da ta dace da addinanmu.

**MAI BA DA LABARI:**
Daga baya a wannan ranar, sai Maigida Ranau Dembele ya zo gidan đan'uwansa, kamar dai yadda a ka tsara. Shi a karkara yake rayuwa. Lokacin da Dauda da Layla suka shiga, sai Fada Bana da Maigida Ranau suka tashi tsaye don girmamawa.

**Fitowa ta 5: A gidan Maigida Ranau Dembele**
Dauda, Maigida Ranau Dembele, Fada Bana, Layla

**DAUDA:** Baba, Kawu, wannan ita ce Layla Umar.

**MAIGIDA RANAU:** Mun yi murna da ganinki, Layla!

**FADA BANA:** Ke ce yayar Hassan?

**LAYLA:** E, ni ce Fada. A madadin mutanen gidanmu ina mai nuna alhini, da ba ka hađuri game da abin da ya faru.

**FADA BANA:** Layla, ƙanenki Hassan da babanki sun zo cocina yau da rana.

**LAYLA:** Sun zo…?

**DAUDA:** …cocinka ma?

**FADA BANA:** Sun zo. Sun nemi na yafe musu. Kuma gaskiya sun mutunta ni. Kuma mun yi addu'a tare. Sannan na gaya musu zan janye ƙarar da na kai Hassan wajen 'yan sanda.

**MAIGIDA RANAU:** Ka kyauta! Na yarda cewa kwanciyar hankali a garin Sodangi ta fi fili muhimmanci.

**LAYLA:** Na gode, Fada! Maigida, ina iya cewa wani abu?

**MAIGIDA RANAU:** Me zai hana? Don Allah zauna! Dauda kai ma zauna! Mu ci gaba da tattaunawa.

**LAYLA:** Ni da Dauda muna da wata shawara.

**MAIGIDA RANAU:** Ta me?

**DAUDA:** Muna son matasan wannan al'umma tamu, da ta ƙunshi Musulmi da Yahudawa da Kiristoci...

**LAYLA:** …dukkan matasan gaba ɗaya…

**DAUDA:** ...su gina wata cibiyar matasa, masu al'adu dabam-dabam a wancan filin. Sai kuma a sa mata suna....

**DAUDA da LAYLA:** …Cibiyar Sabunta Zumunta!

**MAI BA DA LABARI:**

Tafida kuwa tuni ya kwana da sanin cewa wannan rana za ta kawo wani sauyi a rayuwarsa. Wannan sauyin kuwa ba zai rasa nasaba da yadda suka haɗa kansu a Kwalejin Zumunta ba, da kuma yadda suka riƙa tattaunawa a kan tsarin shugabanci, da kuma tunanin samar da mafita ta hanyar lumana. Sannan kuma ga yadda haka kwatsam babansa yake ƙoƙari ya bayyana mishi wani abu da ya daɗe yana damunsa.

**Fitowa ta 6: A gidan su Tafida da daddare**

Tafida, Baban Tafida

**TAFIDA:** Baba, mene ne?

**BABAN TAFIDA:** Kai! Ka ga kuwa kamata ya yi a ce na yaga hoton nan tun tuni.

**TAFIDA:** Wace ce waccan matar? Me ya kawo hotonta teburinka?

**BABAN TAFIDA:** Tafida ke nan. Ai dogon labari ne.

**TAFIDA:** Wai mene ne, Baba? Faɗa min mana!

**BABAN TAFIDA:** *ya fara kuka.*

**MAI GABATARWA:**

To, masu sauraronmu, a nan muke dasa aya a cikin shirin namu na "Ji Ka Karu" a kan "Haɗin kan mutanen Sodangi", inda muka ji yadda Dauda da Layla sun shirya, kuma Hassan ya nemi gafarar Fada Bana. A kasance da mu a shiri na gaba, wato kashi na goma kuma na ƙarshe domin jin abin da ke damun Baban Tafida, da kuma yadda iyayen Dauda da Layla suka karɓi shawarar da suka gabatar musu. Kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo domin sake sauraro ko aiko da tsokaci, wato www.dw-world.de/lbe.